AMPLIFYCHANGE

# KAYAN AIKI

## NA mai kula da tsarin aikin HKLJH



**KUNDIN KOYASWA NA 1 :**

**YADDA ƊAN KASA ZAI ƊAUKI NIYYAR KARFAFA YIN AIKI DA DA DOKA DA AIKIN HKLJH**

Agusta 2019

# Abin da ke ciki

Kalamun farko ..................3
1. **Gabatarwa** ..................5
1.1 **Yanayin da ake ciki** ..................5
1.2 **Dalili** ..................6
1.3 **Manufa** ..................6
1.4 **Guri** ..................6
1.5 **Hanyar tafiyar da aiki** ..................6
1.6 **Abin da kundin koyaswar ya ƙumsa** ..................7
2. **Ma'anar kalmomi** ..................8
2.1 **Ƴan ƙasa** ..................8
2.2 **Masu amfana da aikin** ..................8
2.3 **Niyyar ƴan ƙasa** ..................8
2.4 **Aikin da masu amfana suke yi** ..................8
3. **Matakan sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki** ..................9
3.1 **Neman shawara** ..................9
3.2 **Yin aiki tare** ..................9
3.3 **Sa hannu cikin aiki** ..................9
3.4 **Iya yi wa kai** ..................9
4. **Farilan da ke bida ɗaukar niyyar ɗan ƙasa** ..................11
4.1 **Bisa ga sakamako** ..................11
4.2 **Niyya cikin dukan tsawon lokacin da aikin zai ɗauka** ..................11
4.3 **Ƙarfafa hanyoyin sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki** ..................11
4.4 **Abin da ya yi daidai da yanayin da ake ciki** ..................11
4.5 **Mai bin matakai, da ci gaba** ..................11
5. **Hanyoyin ɗaukar niyya da amfani da su cikin aikin HKLJH** ..................12
6. **Auna muhimmancin ɗaukar niyya game da tsari/projen HKLJH** ..................22
7. **Maƙasudi** ..................25
Abubuwan da ake iya dubawa .................. Erreur ! Signet non défini.

## Kalamun farko

**Ofishin bada Shawara da tallafi ta fannin Tarbiyya daga Tushe da ake kira (CAEB)** ya san da muhimmancin neman afuwa da ƙarfafa iyawar Ƙungiyoyin Fara Hula game da al'amarin kare Hakin mutane, ta fannin Kiyon Lafiya da ya shafi Jima'i da Haifuwa (HKLJH).

An shimfiɗa dokoki da farilai da yawa na ƙasa da ƙasa domin a tabbatar da hakin ɗan Adam gaba ɗaya, da kuma HKLJH daga cikinsu:

- Jerin ayukan cigaba mai ɗorewa daga nan zuwa 2030 ;
- Kundin Majalisar Ɗumkin Duniya da aka sa hannu a kanshi a Francisco a shekara ta 1945
- Yarjejeniya ta ƙasa da ƙasa da ke kula da Hakin Yara Ƙanana da ake kira (CIDE) ta shekara 1990
- Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma na Afirika da aka shirya a shekara ta 1981
- Yarjejeniya ta Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma mai kula da hakin mata a Afirika, da ake kira « Yarjejeniyar Maputo » na shekara ta 2005.

**Ƙarfafa niyyar ɗan ƙasa (NƊƘ)** a cikin aikin tafiyar da tsari/proje, da shugabancin ma'aikatun da ke tafiyar da aikin kiyon lafiya; yana sa ƴan ƙasa su sa kai sosai cikin aikin HKLJH. Sa hannun ƴan ƙasa cikin aikin, ba ya tsayawa ga matakan ƙirƙiro proje ko auna aiki na ƙarshe kaɗai ba. Amma yana tafiya tare da aikin aiwatar da tsari da projen HKLJH. Banda haka, sa hannun ƴan ƙasa cikin ma'ikatun tafiyar da aikin kiyon lafiya, yana tabbata ta wurin niyyar da ta dace da ƴan ƙasa ke ɗauka, abin da zai sa a lura da muryar ƴan ƙasa, da bukatun mutane marasa galihu.

An shirya wannan kundin koyaswa, domin aiwatar da ayukan proje na Amplifychange da ya shafi ƙasashe 4 na Afirika ta kudancin Sahara (Burkina Faso, Guinée, Mali et Niger). Yana ɗaya daga cikin kundayen koyaswa 4 na «Kayan aikin mai kula da tafiyar da aikin HKLJH» wanda za ya ƙarfafa iyawar shugabannin ƙungiyoyi masu aikin neman afuwa, da suke cikin tsarin bunƙasa HKLJH cikin ƙasashen 4 da aka zaɓa a Afirika ta kudancin Sahara. A cikin kafa ƙungiyoyi masu kula da kare hakin mutane game da kiyon lafiya ta fuskar jima'i da haifuwa, wannan kundin koyaswa za ya ƙarfafa aikin haɗin gwiwa tsakanin ƙungiyar fara hula a cikin ƙasa, da wurare daban-daban. Wannan kundayen koyaswa suna cikin kayan aiki:

- Kundin koyaswa na 1: Yadda ƴan ƙasa ke ɗaukar niyya domin ƙarfafa amfanin da dokoki cikin aikin HKLJH
- Kundi koyaswa na 2: A gane, a kuma yi aiki da tsarin da aka yi bisa hakin mutane cikin fannin HKLJH
- Kundin koyaswa na 3: Shimfiɗa aikin haɗin gwiwa domin neman afuwa na samo ma mutane hakinsu, game da aikin HKLJH.
- Kundin koyaswa na 4: Kayan aikin na gwarzayen aikin waye ma mutane kai a kan aikin HKLJH, a cikin makarantu ko wasu wurare daban.

Abin da kundayen koyaswar suka ƙumsa, yana lura da yanayin siyasa, da zamantakewa, da tattalin arziki na ƙasashen, da yankunan ƙasashen, da kuma matsaloli da suka zama kangi ga aikin HKLJH, bisa ga bincike daban-daban da muka yi[1] da kuma abin da abukan aikinmu na cikin sauran ƙasashe suka ji kuma suka gani.

Kowane kundin koyaswa na kayan aiki, an shirya shi yadda za ya zama da sauƙin amfani da shi, inda akwai jagoran koyaswa na kundi cikin siffar PDF da Word, da PowerPoint na kundin, domin bukatun koyaswa nan gaba cikin ƘFH, da bidiyo da aka ɗauka tamkar misali mai kyau na masu koyar da ƘFH.

An shirya kayan aikin cikin harshe faransanci, aka kuma juya su cikin harsuna 4 (Bambaranci na Mali, Maninka na Guinée, Hausa na Niger et Mosanci na Burkina Faso) da kuma rubuntu makafi da ake kira Braille.

Muna fatan wannan kundayen koyaswa za su taimaka ma masu tafiyar da tsarin aiki na ƙungiyoyin da ke aikin bunƙasa HKLJH, su ƙware a cikin aikin kuzarantar da mutane, da sarrafa kuɗi da aka zuba domin kawasda ƙalubalan da suka shafi aikin HKLJH , tare da tabbatar da sa hannun marasa galihu cikin aikin.

[1] Les 11 études menées par Ebenezer International dans le cadre de la présente subvention stratégique sont les suivantes:

- Six (6) Analyse de l'Economie Politique du secteur DSSR respectivement au Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée, Malawi, Zimbabwe, disponible en français. La version Anglaise est aussi disponible pour les études du Malawi et du Zimbabwe ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique de l'Ouest (Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée), disponible en française ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique du Sud-Est (Malawi, Zimbabwe, Ouganda, Afrique du Sud), disponible en français et en anglais ;
- Sondage en ligne sur la satisfaction des citoyens sur les Droits à la santé sexuelle et reproductive pour les écoles secondaires et les universités avec 30 000 répondants dans 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe) disponible en français ;
- Analyse de l'indice du pays favorable aux DSSR pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe), disponible en français;
- Rapport sur la performance des droits à la Santé Sexuelle et Reproductive pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne, disponible en français ;
- Formulaire d'évaluation de la performance des politiques DSSR, disponible en français.

## 1. Gabatarwa

### 1.1 Yanayin da ake ciki

Ƙasashen Afirika ta Yamma da Yankin Kudanci Afirika, suna fuskatanr ƙalubalai da yawa: matsalolin yin aiki da dokoki, matsalolin fassara su, haɓakar ci da haikin mutane, matsalolin da suka zama kangi game da harakar magani, kasawar tabbatar da hakin mutane, rashin isassun kuɗi domin tafiyar da aikin kiyon lafiya, rashin daidaitattun farilai na aikin (HKLJH), bisa ga yadda ƙasashen duniya suka ɗauki alkawari.

AmplifyChange tana da gudummawa mai dubaru da ke da gurin :

- A nemi afuwa, kuma a taimaka wajen inganta siyasa da dubarar aikin HKLJH, dangance da abubuwa (darusa) na kan gaba na AmplifyChange cikin yankunan ƙasashe, cikin ƙasashe 4 na Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso) ;
- A sauƙaƙa ƙarfafa iyawar mutane game da kafa aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyin fara hula, domin iya aiwatar da aiki mafi kyau, bi sau-da-ƙafa na tasirin da siyasar aikin HKLJH cikin ƙasashen 4 na Afirika ta kudancin Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso).

Banda wannan, projen yana aiki tare da ma'aikatu biyu cikin Afirika ta Yamma da Yankin Kudancin Afirika, wato:

- Ƙungiyar Kiyon Lafiya ta Afirika ta Yamma da ake kira (OOAS) a cikin Haɗin Kan Ƙasashen Afirika ta Yamma ta fannin Tattalin Arziki da ake kira (CEDEAO) a Bobo Dioulasso, a ƙasar Burkina Faso;
- Asusun Majalisar Ɗumkin Duniya mai Kula da Al'umma (UNFPA), mai cibiyarsa a Afirika ta Yamma a Dakar, ƙasar Sénégal.

Wannan gudummawa mai dubara ta AmplifyChange aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyi 4 (CAEB, Haɗin gwiwar ƘFH domin sake salon tafiyar da tsarin iyali a Afirika ta Yamma mai aikin da harshen faransanci, Ebenezer International et Humanité & Inclusion) domin tsawon shekara biyu ( 2 ) , daga 1 ga watan Nobamba na 2018 zuwa 31 ga watan Oktoba na 2020, inda **CAEB** ce ke shugabanci. Tana ba ƙungiyoyin da ke cikin wannan ƙawance damar su yi aikin neman afuwa, su kuma tafiyar da ayukan ƙarfafa iyawar ƙungiyoyi domin a inganta siyasar aiki da dubarun HKLJH, cikin ƙasashe 4 na Afrika ta kundanci Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Niger, Guinée da Burkina Faso), tare da kan ziyara ta musanyar bayanai da kwatanta binciken da aka yi cikin ƙasashen Yankin Kudancin Afirika (Malawi, Zimbabwe da Ouganda).

An aiwatar da projen cikin yankunan ƙasashe biyu na Afirika ta kundancin Sahara :

- Afirika ta Yamma: Guinée, Mali, Niger, Burkina Faso ;
- Yankin Kudancin Afirika : Malawi, Zimbabuwe, Ouganda.

### 1.2 Dalili

Ta wannan dalili ne aka shirya waɗannan kundayen koyaswa huɗu na «Kayan aiki na mai kula da tafiyar da tsarinHKLJH ». An zaɓi kundin koyaswa na fa ɗaya (1), da ake kira «Niyyar ɗan ƙasa domin bunƙasa siyasar aikin HKLJH», domin a sa ƴan ƙasa su ɗauki niyyar sa hannu cikin bunƙasa aikin HKLJH ta hanya ashirin da bakwai (27) da ake iya amfani da su bisa ga bukata da kuma yanayin da ake ciki, cikin kowane tsari da proje.

### 1.3 Manufa

Wanan kundin koyaswa na nufin ya sa masu kula da tafiyar da aiki na abukan aikinmu, domin su ɗauki niyya a matsayinsu na ƴan ƙasa, masamman game da abin da ya shafi matakan tsarinsu na HKLJH. Yana ba su hanyoyi ashirin da bakwai na sa ƴan ƙasa ɗaukar niyya wanda daga cikinsu suna iya su zaɓa dangance da gurinsu, da yanayin da suke ciki. Manufar kundin koyaswar shi ne ya tabbatar da sa hannu ƴan ƙasa yadda ya kamata cikin aikin HKLJH, a cikin ƙasashe, jahohi, da gundumomi; a Mali, Guinee, Burkina Faso da Niger.

### 1.4 Guri

Wannan kundi koyaswa yana taimaka ma masu kula da tafiyar da tsarin HKLJH su yi abubuwa kamara haka: :

- Su saba da ɗaukar niyyar ƴan ƙasa, da duk wasu abubuwa da suke da nasaba da haka;
- Gane matakan sa hannu da ƴan ƙasa ke iya yi, da muhimmancinsa cikin aiki HKLJH
- Gane abin da ke bida ɗaukar niyyar ƴan ƙasa da aiki da ita cikin aikin HKLJH;
- A sansance sosai, kuma a auna muhimmancin niyyar ƴan ƙasa cikin tafiyar da tsarin aiki da proje na HKLJH.

### 1.5 Hanyar tafiyar da aiki

A shirya wannan kundin koyaswa bisa ga tafarkin sa hannun kowa da kowa, daidai da wannan hanyar tafiyar da aiki, mai matakai huɗu :

- **Mataki na 1 :** zaɓen mashahurin da za ya ƙirƙiro kundin farko;
- **Mataki na 2 :** Neman littattafai da munsanyar bayanai tsakanin jigajigan masu akin cikin HKLJH;
- **Mataki na 3 :** Yin amfani da shawarwari da aka samu cikin binciken da aka tafiyar da shi ƙarƙashin Ebenezer International;
- **Mataki na 4 :** Yin amfani da ƙarin bayanai da aka samu cikin wallafawar ƙarshe ta kundin.

### 1.6 Abin da kundin koyaswar ya ƙumsa

An tsara abin da kundin koyaswar ya ƙumsa, da sashe uku na koyaswa kamar haka:

- **Sashe na 1 : Ma'anar kalamomi**

Tana bada ma'anar ko minene ɗan ƙasa, masu amfana da aikin, niyyar ɗan ƙasa, da aikin da masu amfana da aikin za su yi.

- **Sashe na 2 : Matakai na yadda ƴan ƙasa za su sa hannu cikin aiki**

Wannan sashe yana bada ma'anar shawara, aiki tare, sa hannu cikin aiki da iya yi wa kai, cikin matakan sa hannu na ƴan ƙasa cikin aiki.

- **Sashe na 3 : Abubuwan da ke bida ɗaukar niyyar ƴan ƙasa**

Wannan sashe yana gabatar da yadda ake aiki da farilai biyar (5) masu bida ɗaukar niyyar ƴan ƙasa ta fuskar HKLJH, wato : maida hankali ga sakamako, niyya cikin aiki duk tsawon da aikin zai ɗauka, ƙarfafa sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki, yin amfani da yanayin da ake ciki, da cigaban aiki.

- **Sashe na 4 : Yadda ƴan ƙasa ke ɗaukar niyya, da aiki da ita cikin HKLJH**

Sashen yana bada ƙayyadaddar ma'ana kowace hanya daga cikin hanyoyi 27 na ɗaukar niyyar ɗan ƙasa, yana kuma bada misalai na yadda ake iya amfani da kowanensu. Wannan yana buɗe ƙofa ga masu kula da tafiyar da aiki su kawo wani abu sabo cikin aiwatar da tsari/proje na HKLJH.

- **Sashe na 5 : Auna muhimmancin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa**

Wannan sashe na gabatar da tambayoyi da wani allo na auna muhimmancin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa cikin aikin HKLJH. Yana sa masu tafiyar da tsarin aikin HKLJH su ga darajar sa wata hanya da ta kamata na ɗaukar niyyar ɗan ƙasa cikin wani aiki, a kuma auna a gani adadin kuɗin da za a kashe domin aikin.

## 2. Ma'anar kalmomi

### 2.1 Ƴan ƙasa

**Ƴan ƙasa su ne waɗanda suke amfana da aiki, da gwamnati ko wasu ma'aikatun cigba, da kuma ma'aikatu masu zaman kansu ke yi a cikin ƙasa.** Ƴan ƙasa suna iya su yi wani abu guda-gudansu ko su tsara kansu cikin ƙungiyoyi kamar irin su ƙungiyar mata, ƙugiyar ƴan gari. Ƙungiyoyin Fara Hula (ƘFH) suna iya su wakilci ƴan ƙasa, kuma suna iya su haɗa da wasu ƙungiyoyi daban da ba sa aikin neman riba, kamar iri su Ƙungiyoyi Masu Zaman KANSU (ONG), ƙungiyoyi masu bada taimako, ƙungiyoyin addini, ƙungiyoyin masu hannu da shuni, Jami'o'i, makarantu masu shimfiɗa siyasar aiki da bincike, sandika, da wasu sassan al'umma da suka tsara kansu. A cikin irin wannan yanayi, ba ana amfani da kalmar ɗan ƙasa ta fuskar doka ba ne, amma ana nufin kowane mutum. Ana nufin duk wanda ke cikin wata al'umma ko ƙasa banda wani bambanci ko wariya.

### 2.2 Masu amfana da aikin

Masu amfana da aikin, su ne wasu daga cikin ƴan ƙasa da aka nufa da wani tsari/proje na cigaba, da ake ganin za su iya more ma projen. Misali: tsari/projen na Tsarin Iyali mai neman inganta samun kulawa, na iya samun ƙungiyoyin matasa da na mata marasa galihu a cikin karkara tamkar masu amfana da aikin.

### 2.3 Niyyar ƴan ƙasa

Niyyar ƴan ƙasa ya zama aikin da ƴan ƙasa da gwamnati, ko ma'aikatu masu ƴancin kansu suke yi cikin aiwatar ayuka (taɗi a kan siyasa, tsare-tsare, proje, sashen masu bada shawara da yin nazari), da yake ba ƴan ƙasa wani marmari cikin ɗaukar ƙuduri na inganta sakamako aikin da ake yi.

### 2.4 Aikin da masu amfana suke yi

Aikin da masu amfana ke yi, shi ne irin niyyar da ƴan ƙasa ke ɗauka, yana kuma nufin (neman shawara, yin aiki tare da iya yi wa kai), tare da ƴan ƙasa da suka tabbata masu morewa aikin da ake yi (kai tsaye) lokacin shiri, da aiwatarwa, da auna aiki. Gurin shi ne a sa wasu ayuka na neman shawara, aiki tare da iya yi wa kai cikin ƙirƙiro proje da aiwatar da shi, domin a sauƙaƙa koyo na yau da gobe, a inganta bin sau-da-ƙafa na proje, domin a sami sakamako mafi kyau.

## 3. Matakan sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki

Matakan sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki sun ƙumshi neman shawara, aiki tare da sa hannu cikin aiki, da iya yi wa kai (a dubi hoto na 1.1).

### 3.1 Neman shawara

Neman shawara shi ne «a tambayi wani ya bada ra'ayinsa » 2. Misali, ana iya a nemi shawarar al'umma ta wurin jefa kuri'a

Wannan yana nufi bayani daga wajen al'umma ko waɗanda aka tambaya, wanda wani lokaci yana bukatar a koyar da mutane, a bada fassara, a kuma a daidaita wasu abubuwa.

### 3.2 Yin aiki tare

Yin aiki tare da wasu, sa hannu cikin wani aiki tare da wasu. Wannan mataki yana bukatar a koyar da abukan aiki, dole kuma waɗanda suka shirya aikin ya zamana suna da cikakkar dama, domin su rakka sauran waɗanda abin ya shafa ta wurin musanyar bayanai lokaci zuwa lokaci.

### 3.3 Sa hannu cikin aiki

Sa hannu cikin aiki shi ne mutum ya bada tasa gudummawa cikin aiki. **[3]**. Cikin fannin siyasa, da zamantakewa, rayuwa tare, sa hannu cikin aiki ya zama tamkar *«sa albarkacin baki cikin tattaunawa da ƙudurin da ya shafi ƙungiya, siyasa ta gaba ɗaya da makomar al'umma. ».*

### 3.4 Iya yi wa kai

Iya yi wa kai shi ne, mutum ya iya yi wa kansa komi, ya samo wa kansa ƴanci kansa.[4]. Ana faɗin wannan zuwa ga ma'aikata ko ƙungiya da take tafiyar da aikinta da kanta. Shi ne alamar ƙungiyoyi da suke da ƴanci kansu, da kuma suke iya su yi abin da suke so ba tare da wani ya agaza masu ba..


---

[2] https://www.larousse.fr/dictionnaires/francais/consultation/18521

[3] https://www.lalanguefrancaise.com/dictionnaire/definition-participation/

[4] https://www.larousse.fr/dictionnaires/francais/autonomisation/6780

Hoto na 1 : **Yadda ɗan ƙasa ke ɗaukar niyya**[5]




1. Bada bayani: A ba ƴan ƙasa daidaitattun bayanai na gaske domin a taimake su su gane matsalar da ake ciki, da mafita, da damar warware matsalar
2. Neman shawara : samun ra'ayoyin wasu dangance da nazari, da mafita, da ƙudurin da aka ɗauka
3. Yin aiki tare : Kafa hulɗar aiki tare da ƴan ƙasa dangance da wani sashe na ɗaukar ƙuduri, ko dukan ƙudurin gaba ɗaya.
4. Iya yi wa kai : Ɗaukar ƙuduri na ƙarshe yana cikin hannun ƴan ƙasa

[5] *Source:* Adapté de « IAP2 Spectrum of Public Participation», Association internationale pour la participation publique.

## 4. Farilan da ke bida ɗaukar niyyar ɗan ƙasa

A cikin tsari da proje na HKLJH, ɗaukar niyya daga ɗan ƙasa, tana dogara ga manyan farilai biyar : bisa ga sakamako, niyyar ta dukan tsawon aikin, ƙarfafa hanyoyin ɗaukar niyyar, tafiya bisa ga yanayin da ake ciki, da cigaba.

### 4.1 Bisa ga sakamako

Niyyar ɗan ƙasa tana da nata tamani; wannan yana bukatar a bada kayan aiki, lokaci, da ƙoƙari domin a iya ƙirkirowa kuma a aiwatar da hanyoyin da suka kamata. Ta dalilin haka, ya kamata a zuba jari cikin aikin ƙarfafa iyawar mutane domin su iya kai ga inganta sakamakon tsari/proje na HKLJH. Iya tafiyar da irin wannan aiki, yana bukatar a san ma'aikatan da ke cikin a'amarin kiyon lafiya (cikin ƙasa, cikin jahohi, gundumomi), inda niyyar ƴan ƙasa za ta iya kawo gudummawa mai ƙarfi cikin sakamakon da za a samu, a ƙayyade a sarari ko minene gurin da ake da shi, game da sa hannun ƴan ƙasa cikin ƙayyadadden yanayi.

### 4.2 Niyya cikin dukan tsawon lokacin da aikin zai ɗauka

Ko da shike ana neman shawarwari a lokacin shirya tsare-tsare da proje na HKLJH, ɗaukar niyya ba ya zama abin da ake yi take-yanke ba a lokacin aiwatar da aiki. Bunƙasa hanyoyin ɗaukar niyya ƴan kasa cikin tsare-tsare/projen HKLJH, yana hangen ƙara ƙarfafa iyawar mutane a lokacin shiri da aiwatar da aiki, da auna tsare-tsaren da projen, domin a kai ga inganta sakamakon da za a samu.

### 4.3 Ƙarfafa hanyoyin sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki

Ƙoƙarin bunƙasa niyyar ƴan ƙasa, yana nufin ƙafafawar hanyoyin irin na gwamnati da za su sa ƴan ƙasa su sa hannu cikin aiki. A cikin kowane tsari/proje na HKLJH ko na tafiyar da ma'aikatun kioyon lafiya a matakai daban-daban, masu kula da tafiyar da tsari/proje na bukatar su tsaida magana tare da ma'aikatun gwamnati ko na wuri a kan yanayin da zai kyautata ɗaukar niyyar ƴan ƙasa.

### 4.4 Abin da ya yi daidai da yanayin da ake ciki

A cikin tsare-tsare/poje na HKLJH, dole niyyar ƴan ƙasa ta yi daidai da dokoki da ka'idodin ƙasa, du kuma duk wasu matakai da ke akwai. Ya kamata ya lura da iyawar mutane a matakai daban-daban, da yardar gwamnati ko hukumar wuri, da kuma ƴan ƙasa su ɗauki niyya. Ya kamata gwamnati ta ba ƴan ƙasa bayanai masu muhimmanci irin yadda za su same su da sauƙi, kuma su gane, kuma a ƙarfafa iyawar mutane da hanyoyi bada amsoshin da suka dace dangance da ƙarin bayanai da ƴan ƙasa suke badawa. Ya kamata ƴan ƙasa su zama da isasshen sanin yadda za su sa hannun cikin aiki, su kuma taimaka sosai wajen cimma sakamakon aikin HKLJH.

### 4.5 Mai bin matakai, da ci gaba

Ta dalilin wuya al'amarin ɗaukar niyyar ɗan ƙasa, da lokacin za a ɗauka domin a kai ga sa mutane su sa hannu cikin aikin iri yadda ya kamata, a inda babu shi, da bukatar cigaba da koyo, ana bada shawarar a bi matakai na shigar da niyyar ƴan ƙasa cikin tafiyar aikin tsari/projen HKLJH. Ana fatan a auna sakamakon cigaba da darasin da aka koya cikin amfani da hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa kowane wata shida, domin a kafa hanyar koyo mai bin matakai, mai ci gaba, domin a kawo cin gyara tare da lura da yadda yanayin yake sakewa.

## 5. Hanyoyin ɗaukar niyya da amfani da su cikin aikin HKLJH

Wannan allo yana gabatar da hanyoyi ashirin da bakwai (27) na ɗaukar niyyar ƴan ƙasa, wanda ana iya kasa su cikin rukuni huɗu :

a) Hanyoyin gargajiya na neman shawara da mayar da bayanai, kamar misalin gungun tattaunawa da binciken samun gamsuwa;
b) Hanyoyin sa hannun kowa da kowa, kamar misalin katin auna aiki na a'lumma, tsari kasafin kuɗi inda kowa ya sa hannusa.
c) Hanyoyin da ƴan ƙasa suke bidawa, kamar misalin komitotin tafiyar da aiki na al'umma, ko na masu kula da masu amfana da aikin ;
d) Hanyoyin bincike da lura daga wasu daban sun ƙumshi binciken sha'anin zamantakewa, katin auna aiki na ɗan ƙasa, binciken yadda aka kashe kuɗin jama'a, da yin aiki tare da wasu masu bincike da lura masu zaman kansu, irin su kafofin bada bayanai, matsakanta ko manyan ma'aikatun bincike da lura.

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma'ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| 1. **Taron waye kan jama'a a kan kasafin kuɗi** | **Taron waye kan jama'a a kan kasafin kuɗi** ƙoƙari ne mai yawa – wanda yawanci lokaci ƙungiyar fara hula ce, da ma'aikatan jami'a, ko wasu ma'aikatun binciken ilimi ne suke yin shi, domin a ƙarfafa iyawar ƴan ƙasa da ƙungiyar fara hula domin su fahimci ko minene kasafin kuɗi, su nemi gwamnati ya bada lissafi game da niyyar da ya ɗauka game da kasafin kuɗin ƙasa, su kuma faɗa a ji cikin abubuwan da ya kamata kasafin kuɗin ya ƙumsa. | • Koyaswa ko waye ma ƙungiyoyin fara hula kai bisa ga sha'anin kasafin kuɗi na ƙasa, na jaha, ko na guduma<br>• Koyaswa ko waye ma ƙungiyoyi fara hula kai a matakai daban-daban na shirya kasafin kuɗi, a Ofishin Ministan kiyon lafiya da Tsabta*, a gidajen likita na masaman,* da gidajen likita na jahohi, da ƙananan gidajen likita na gudumomi, da ASACO-CSCom da gidanjen likita na karɓar haifuwa a cikin karkara<br>• Horasda ƙungiyoyin fara hula bisa ga nazari da shirin kasafin kuɗi na ƙasa gaba ɗaya, da Tsarin Aikin Ƙasa mai Kasafin kuɗi( PANB) masamman<br>• Tallafi zuwa ga masu kula da fusahar aiki na gwamnati domin a wallafa kuma a yaɗa bayanai da alamun kasafin kuɗin dalla-dalla da suka shafi kiyon lafiya ta fannin HKLJH<br>• Horasda masu kula da fusahar aiki na gwamnati game da kasafin kuɗi mai nasaba da al'amarin jinsi da |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma'ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | | tabbatar da adalci cikin aikin HKLJH<br>• Shimfiɗa hanyar bidawa da rubuta rahoto a kai-a kai game da kuɗin da ake kashewa ta fannin kiyon lafiya a matakai daban daban na shugabancin ma'aikatun kiyon lafiya |
| 2. **Kundin ƴan ƙasa** | Ƙundin ƴan ƙasa, wani littafi ne da yake sanas da ƴan ƙasa game da hakinsu da ya shafi kulawa da jama'a a matsayinsu na masu samun kulawar; da irin farilan ya kamata a kiyaye ta wannan fanni (tsawon lokaci da inganci); da samun damar kan ƙara idan ba a kiyaye farilan ba, da matakan da ya kamata a bi, da kuɗin da ya kamata a biya domin samun kulawa. Kundaye suna ba masu amfani da su ƴanci su nemi fassara (da abin shafe hawaye cikin wani yanayi) idan ba a kiyaye farilan ba. | • Sa hannu a ka kundayen ƴan ƙasa tsakanin ƙungiyoyin fara hula da suke aiki cikin fannin kiyon lafiya da ma'aikatun kiyon lafiya na gwamnati a matakai daban daban na aikinsu a matsayinsu na ƙungiyoyi masu zaman kansu, ƙungiyoyi ko gungun mutane da suka tsara kansu...<br>• Sa hannu a kan kundayen ƴan ƙasa tsakanin wakilan masu morewa da kulawa da lafiyarsu, gidajen likita, sanannun gidaje likita( CSRef), ASOCO-CSCom… ta wurin maida hankali ga aikin HKLJH, tare da bada rahoto kowace shekara a kan cigaban aiki, da sabunta sa hannu a kan kudin kowaɗanne shekaru biyu (2) |
| 3. **Katin auna aiki na ƴan ƙasa** | **Katin auna aiki na ƴan ƙasa** shi ne auna aikin yadda ma'aikata suke kulawa da mutane (ƴan ƙasa) ta wurin tambayar waɗanda aka kula da su. Wannan ya wuce sha'anin tattara bayanai, ya zama wani makami na neman bada lissafi ta wurin amfani da kafofin yaɗa labarai da neman afuwa da ƙungiyar fara hula take yi, da yake rakka aiki. | • Tsara tambayoyi lokaci zuwa lokaci ta hanyar yanar gizo ko bisa takarda zuwa ga masu samun kulawa ta fannin kiyon lafiya cikin gidajen likita, sanannun gidajen likita (CSRef), ASOCO-CSCom da yaɗa sakamakon cikin kafofin yaɗa labarai.<br>• Bincke na masamman a wurin marasa galihu da aka ware, waɗanda ba su iya zuwa wurin samun kulawa ta fannin HKLJH a cikin gidajen likita, sanannun gidajen likita (CSRef), ASOCO-CSCom da yaɗa sakamakon binciken cikin kafofin yaɗa labarai. |
| 4. **Bincike na gamsuwa daga ƴan ƙasa** | **Binciken gamsuwa daga ƴan ƙasa** yana auna ingancin aikin gwamnati da kulawa da ake badawa bisa ga yadda ƴan ƙasa suka ji, kuma suka gani. Dangance da | • Auna ingancin aikin masu fusahar tafiyar da aiki da ma'aikatun kiyon lafiya na gwamnati.<br>• Sansancewa da abubuwan kan gaba na proje da dubarun samun wurin gina ma'aikata domin aikin |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma'ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | guri, binciken na iya tattara bayanai a kan darasi daban daban, daga irin yadda mutane suke gani tafiyar da aiki kulawa da su, da zaɓaɓɓun wakilai, da marmarin samun sabbin proje, da wuraren aiki. | HKLJH daga ƴan ƙasa, tare da maida hankali masamman ga gungun marasa galihu |
| 5. **Goyon bayan ƴan ƙasa da waɗanda suka amfana zuwa ga masu ɗaukar ƙuduri** | **Goyon bayan ƙasa da waɗanda suka amfana zuwa ga masu ɗaukar ƙuduri,** hanya ce ta tabbatar da neman bada lissafi ta wurin yardar ma mutanen da ke iya ƙarfafa masu amfana su sami shiga cikin komitoti da suke ɗaukar ƙuduri, dangance da ayukan proje da ake tafiyar da shi (kayan aikin proje) ko na mashawartan ma'aikatu (kayan aiki na wani fanni). | • Horasda ƙungiyoyin fara hula a kan dokokin da ke tafiyar da sassan shugabanci da tafiyar da aiki cikin ma'aikatun gwamnati, daga na ƙasa gaba ɗaya zuwa na gundumomi;<br>• Horasda wakilan ƙungiya fara hula a kan sassan kula da aiki da shugabancin ma'aikatun kiyon lafiya, da sanin ko minene shugabanci, yi aikin cikin haske, adalci zuwa ga kowane jinsi, tare da maida hankali ga lura da abubuwan kan gaba na aikin projen HKLJH<br>• Wakilcin ƙungiyar fara hula cikin komitotin tafiyar da aiki ko bida tsare-tsare da projen HKLJH |
| 6. **Ƴan ƙasa masu kula da auna aiki** | **Masu auna aiki,** su ne mutanen da aka zaɓa cikin al'umma, waɗanda ke bada shawarwari ko hanyoyin sa hannu da za su sa cika matakan siyasa. | • Kafa masu auna aiki domin su shirya shawarwari zuwa ga hukumomi a matakai daban daban na shimfiɗa siyasar aiki da kasafin kuɗi na HKLJH<br>• Aza masu auna aiki domin su duba kuma su shirya shawarwari zuwa hukumomi a matakai daban daban ta bayan bada rahotanni a kan aikin HKLJH |
| 7. **Bada kwangila daga al'umma** | **Al'umma tana bada kwangila** a lokacin da mutanen gari ne ƴan kwangila, ko lokacin da wasu gungun mutane suna hayar wasu ƴan kwangila domin aikin gine-gine. | • Bada horaswa da bada wajibi ga al'umma a kan matakan gina ma'aikatu na kiyon lafiya da sayen kayan aiki<br>• Bada horaswa da wajibi ga al'umma a kan yadda ake tafiyarda aiki tare , da kan marasa lafiya a likita mafi girma cikin gaugawa, masamman daga ƙauye, zuwa wasu gidajen likita |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma’ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | | • Horaswa da bada wajibi ga al’umma cikin sana’ar saye da saidawa magunguna, masamman waɗanda suka shafi bukatun kiyon lafiya ta fannin haifuwa<br>• Horaswa da bada wajibi ga al’umma cikin aikin bada kwangila ga masu kula da aikin HKLJH, masamman cikin ƙauyuka |
| 8. **Tafiyar da aikin al’umma** | **Ana zance tafiyar da aikin al’umma** lokacin da ƴan gari ne suke tafiyar dukan aikace-aikace, ko kuma su ne suke riƙe da su. Masu amfana da ayukan su ne kuma masu galihun aikin (kowane mai amfana da aikin yana da nasa rabo idan aka kafa masana’antu na haɗin gwiwa). | • Horasda al’umma a kan shugabanci na ƙwarai cikin ƙungiyoyin kiyon lafiya<br>• Horasda shugabannin al’umma da ke cikin shugabancin ƙungiyoyin kiyon lafiya, a kan farilan bada kwangila, bin sau-da-ƙafa na kwangilar, da lura sosai a kan abin da ya shafi aiki ko magani na HKLJH<br>• Horasda shuagabannin al’umma da suke aiki cikin ƙungiyoyin kiyon lafiya, a kan yadda ake tanadawa da sarrafa kayan aikin ƙungiyoyin |
| 9. **Bin sau-da-ƙafa na al’umma** | **Bin sau-da-ƙafa** da al’umma ke yi, wata hanya ce ta tattarawa da adanawa, da nazarin bayanai; hanya ce ta sadarwa da aikatawa bisa ga bayanai da aka samu domin a inganta aiki. Yana sa a nemi bada lissafi ga ma’aikatun gwamnati a kan abin da suka aikata, a bada bayanai, a yaɗa sakamakon bin sau-da-ƙafa, a gano /a kuma ɗauki matakan horo, a kuma nemi sauƙaƙa taɗi tsakanin ƴan ƙasa da shugabannin proje. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar bin sau-da-ƙafa da al’umma ke yi na ma’aikatun kiyon lafiya, a matakai daban-daban a cikin ƙauyuka da birane<br>• A shirya alamu da yadda za a tafiyar da aiki bin sau-da-ƙafa na ma’aikatun kiyon lafiya a matakai daban-daban<br>• A shirya hanyoyin neman bada lissafi a kai a kai, na shugabannin ma’aikatun kiyon lafiya, zuwa ga mutanen da suka amfana, da kuma masamman ma’aikata da masu kula da sha’anin magani na HKLJH |
| 10. **Lura da ayuka cikin al’umma** | **Lura da ayuka da al’umma ke yi** shi ne lura da ayukan proje na gine-gine da ƴan ƙasa da ƙungiyoyin al’umma suke yi inda suka zuba jarin kuɗi, inda suka sa hannu gadan-gadan ko ta wata hanya na neman | • A fassara kum a yaɗa ma’anar lura da al’umma ke yi a kan tsarin HKLJH a dukan matakai.<br>• Sa bakin kafofin yaɗa labarai na gargajiya cikin tattaunawa da ake a kan yadda al’umma ke lura da ayuka da ake aiwatar da su ta fannin HKLJH a dukan matakai |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma’ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | a bada lissafi. Ana yi wannan a dukan matakai na proje, ko da an fi maida hankali ga aikin gine-gine. | |
| 11. **Allon al’umma na bin sau-da-ƙafa** | **Allon al’umma na bin sau-da-ƙafa** hanya ce ta auna aikin gwamnati da al’umma ke amfani da ita, ta wurin nazarin inganci bayanai da aka samu cikin tattaunawa da aka yi tare da al’umma. Yawancin lokaci ya ƙumshi taruwanni da ake yi tsakanin masu yin aiki da masu amfana da aiki, domin a yi tsarin warware matsaloli ko kasawa da aka samu. | • A fassara kuma yaɗa ma’anar allon bin sau-da-ƙafa na al’umma a matakai daban-daban, na aikin kiyon lafiya da tsari ko projen HKLJH cikin al’umma da ƙungiyoyin fara hula<br>• A horasda shugabannin al’umma da na ƙungiyoyin fara hula a kan aikin bin sau-da-ƙafa da nazarin bayanai a kan tsari da projen HKLJH<br>• A fassara kuma a yaɗa ma’anar « taɗi cikin gungun mutane » zuwa ga ma’aikata da masu amfana da aikin; tare da shirya tsarin ayukan da za a yi tare, aka kuma bi su sau-da-ƙafa |
| 12. **Neman shawara** | **Neman shawara**, da ya bambanta da tattaunawa, munsanyar magana ne inda mai neman shawarar yana ɗaukar niyyar ya “saurara sosai”, ya kuma yi nazari a hankali kwance, ƙarin bayanai da tunani, da shawarwarin da ya samu. Shawarwari a kan nagargarun tabi’u, suna mayar da bayanai a kan abin da aka ji, da abin da aka sa ko aka manta, da kuma dalilan da suka sa shawarwarin za su taimaka wajen inganta siyasar aiki da tsari. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar neman shawara game da aikin HKLJH cikin ƙungiyoyin fara hula da shugabannin al’umma.<br>• A shirya taruwannin neman sharwara na kowa da kowa lokaci zuwa lokaci a kan yadda ma’aikatun kiyon lafiya suke aiki a kowane mataki |
| 13. **Tattaunawa a cikin gungun mutane** | **Tattaunawa a cikin gungun mutane** ana shirya su da guri, da tsari, da lokaci, da matakai na masamman. Gungun mutanen ya ƙumshi ƙalilan sassa da za su tattauna a kan tasiri da damuwa da ke akwai cikin aikin proje, domin a bada | • A fassara kuma a horas da mutane a kan ma’anar tattaunawa cikin gungu, cikin ƙugiyar fara hula da shugabannin al’umma<br>• A shigar da tattaunawa da ake yi cikin matakan bin sau-da-ƙafa na tsari da projen HKLJH<br>• Kafofin yaɗa labarai na gargajiya su yaɗa sakamako ko maƙasudin tattaunawar da aka yi cikin gungun mutane |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma'ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | shawarwari. An shirya su domin a auna yadda mutane suke ganin ayukan da aka aiwatar da su, domin kuma a sami fahimta cikakka game da hangen gaba, da sanin ya kamata, da damuwar da waɗanda aikin ya shafa suke da. | game da aikin bin sau-da-ƙafa na tsari da projen HKLJH |
| 14. **Hanyoyin kan ƙara (yadda ake kula da mutane idan ba su yarda ba, a kan wani al'amari)** | **Hanyoyin kan ƙara** hanya ce wadda ake bi domin a bada amsa ga tamabaya ko neman ƙarin bayani dangance da aikin proje, warware matsalolin da aka samu, da kuma damuwar da aka kawas da ita yadda ya kamata | • A shirya fili ko shafi ta hanyar yanar gizo da za ba mutane damar su sanas da hukuma a duk lokacin da suka ga akwai wata tangarɗa a cikin aikin HKLJH , kuma su nemi hukuma ta yi sauri ta kula da al'amarin<br>• Kafofin yaɗa labarai su lura kuma su bada rahoto lokaci zuwa lokaci a kan yadda aka kula da irin ƙarar da aka kai a matakai daban daban<br>• Karfafa ma'aikatan gwamnati masu fusahar tafiyar da aiki, domin a iya kula da ƙarar da mutane suke kawowa game da aikin HKLJH |
| 15. **Nazarin kasafin kuɗi daga wata ƙungiya mai ƴancin kanta** | **Nazarin kasafin kuɗi**, mataki ne inda mambobin ƙungiyoyin fara hula suke nema su fassara, su lura, kuma su yaɗa bayanai dangance da kashe-kashen kuɗi da jari da aka zuba, domin a samo kuɗi daga kasafin kuɗi da aka shirya. | • A fassara kuma a yaɗa ma'anar nazarin kasfin kuɗi a cikin ƙungiyoyin siyasa da suke aikin cikin fannin HKLJH<br>• A tafiyar da nazarin kasafin kuɗi a kan kasafin kuɗin ma'aikatun kiyon lafiya, da tsari ko proje na HKLJH, tare da yaɗa sakamakon nazarin da aka yi.<br>• Horasda ƙungiyoyin fara hula a kan yadda ake shirya kundin neman afuwa dangance da aikin HKLJH wurin hukumomi da ya kamata a cikin ƙasa da gundumomi |
| 16. **Bin sau-da-ƙafa na abin da ke shigowa** | **Bin sau-da-ƙafa** shi ne a lura da duk wasu kayan aiki da za su shigo cikin ƙasa ko wani wuri. Wannan shi ne ake kira bin sau-da-ƙafa na kayan aiki. | • A fassara kuma a yaɗa ma'anar bin sau-da-ƙafa na abubuwan da ke shiga (kayan aiki ko aiki) cikin al'umma da ƙungiyoyin fara hula da suke cikin tafiyar da aiki da tsari, da proje na HKLJH<br>• A shimfiɗa hanyoyin bin sau-da-ƙafa na abubuwan da ke shigowa, da tsari, da proje na HKLJH da ake aunawa kowane wata uku, ko shida |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma’ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| 17. **Wa’adin yin aiki cikin sahihanci** | **Wa’adin yin aiki cikin sahihanci,** hanya ce ta yin komi a sarari da mutane ke bi domin ƙayyade ka’idodin da za a bi na bada kwangila. Ya ƙumshi «niyyar yin komi cikin sahihancin zuci» inda waɗanda ke cikin aikin suna ɗaukar niyyar ba za su karɓi cin hanci da rashawa ba. Masu neman kwangilar ba za su yarda su yi abin da zai tilasa a ba su kwangilar ba; idan kuma suka sami kwangilar, ba za su yi aiki da ha’inci ba | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar wa’adin yin aiki da sahihanci cikin ma’aikatun gwamnati da ƙungiyar fara hula, da masu aiki cikin HKLJH, a cikin matakai daban daban na ma’aikatun kiyon lafiya<br>• A shimfiɗa hanyoyin bin sau-da-ƙafa lokaci zuwa lokaci a kan yadda ake aiki da wa’adin da aka yi na aiki cikin sahihanci cikin matakai daban daban na ma’aikatun kiyon lafiya. |
| 18. **Yin kasafin kuɗi tare** | **Yin kasafin kuɗi tare** hanya ce da ƴan ƙasa ke sa bakinsu cikin shirin kasafin kuɗi kai tsaye, da ɗaukar ƙuduri, da bin sau-da-ƙafa na kasafin kuɗin. Wannan yana sa ƴan ƙasa su iya sa a saurare su, game da abin da suke so a sa cikin rukunin kan gaba. | • A bunƙasa yin kasafin kuɗi tare, a kuma tabbatar da cewa marasa galihu su ma an dama da su. (masamman matasa, mata, da nakkasassu) a cikin dukan matakai na ma’aikatun kiyon lafiya<br>• A sanas da taruwanni na shirya kasafin kuɗi tare, tare da maida hankali ga abin da ya shafi bukatun aikin HKLJH |
| 19. **Binciken kayan aiki** | **Binciken kayan aiki** ya shafi mambobin al’umma da suke lura da kayan aiki a inda proje ya kafa ma’aikatarsa, masamman a inda babu mashahuran masu bincike domin su duba tsarin kayan aikin. Ƴan ƙasa suna auna ingancin kayan da aka yi amfani da su cikin gine-gine. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar yin binciken kasancewar kayan aiki tare cikin ƙungiyoyin fara hula da al’umma;<br>• A shirya matakan tafiyar da binciken kayan aiki, wanda al’umma da ƙungiyoyin fara hula ke iya ganewa kuma su yi amfani da shi, wanda ya yi daidai da matakan ma’aikatun kiyon lafiya<br>• A yaɗa rahoton binciken da aka tafiyar da shi a kan aikin HKLJH |
| 20. **Tsarin aiki tare** | **Tsarin aiki tare** yana haɗa ɓangare daban daban, domin su auna su gani yadda yanayi ya kasance, domin a shirya dubarun da suka dace domin a warware | • A fassara a kuma yaɗa ma’anar shirya tsari tare cikin aiki da tsari, da proje na HKLJH a dukan matakai na ƙasa gaba ɗaya da na wuri<br>• Horasda shugabannin al’umma da ƙungiyoyin fara hula |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma'ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | matsalolin da aka gano da su tare. Ana shirya sassa, da guri, da dubarun proje bisa ga akidar aiki tare duk waɗanda abin ya shafa. | a kan siyasar aiki da tsari, da yadda ake shimfiɗa guri, da ayukan bunƙasa HKLJH a lokutan shirya tsarin aiki tare a matakai daban daban na shugabanci ma'aikatun kiyon lafiya |
| 21. **Binciken abubuwan da ake saye** | **Binciken abubuwan da ake saye,** bincike ne da wani na waje ke yi a kan shagalin saye-sayen da mutane ke yi, al'umma da ƙungiyoyin fara hula, domin a tabbatar ba keta dokokin sayen kaya ba. | • A fassara kuma a yaɗa ma'anar binciken al'amarin saye-saye zuwa ga masu sa hannu cikin aikin HKLJH, masamman ƙungiyoyin fara hula<br>• Horasda ƘFH da ke aikin cikin HKLJH a kan matakan sayen kaya.<br>• Bincike na lokaci zuwa lokaci na abubuwan da ake saye domin aikin HKLJH, da kuma yaɗa sakamakon binciken ta kafofin yaɗa labarai. |
| 22. **Yaɗa bayanai domin sanar da kowa** | **Yaɗa bayanai domin sanar da kowa** shi ne yaɗa bayanai daga gwamnati, bisa ga aikin proje a wurare daban daban inda kowa ke iya ganinsu, ko cikin ma'aikatun gwamnati, makarantu, da gidajen likita, a cibiyoyin proje, da cikin gari, ko wuraren da mutane ke gamuwa su tattauna a kan abin ya shafi gwamnati. | • A fassara kuma a yaɗa ma'anar yaɗa bayanai ko'ina domin a sanar da mutane game da aikin HKLJH, zuwa ga duka waɗanda ke da hannu cikin aikin da al'ummar da ke amfana da aikin HKLJH<br>• A gano da wurare da suka dace domin a yaɗa bayanan aikin HKLJH, saboda mutane su duba lokaci zuwa lokaci<br>• Masu aikin cikin HKLJH su shirya ka'idodin cikin gida na amfani da bayanan da ke kakkafawa domin mutane su gani, inda za sanas da kowa a kan farilan amfani da bayanan da aka kakkafa bisa ga aikin HKLJH cikin al'umma |
| 23. **Binciken a kan bin sau-da-ƙafa na kuɗin da aka kashe cikin aiki (ESDP)** | **Irin wannan bincike (ESDP)** ya ƙumshi ƴan ƙasa da suke lura da yadda ake shiga da fita da kayan aiki na mutane domin a kula da su, daga farko zuwa ƙarshe. Wannan yana iya sa a gano da abin da ke hana ruwa gudu cikin aiki, kasawa, da cin hanci da rashawa. | • A fassara kuma a yaɗa ma'anar binciken shiga da fita na kayan aiki( ESDP) cikin waɗanda ke abukan aiki cikin HKLJH<br>• A tafiyar da wannan bincike cikin HKLJH daga matakin ƙasa gaba ɗaya zuwa na wurare, wanda ƘFH za su yi, a kuma yaɗa sakamako cikin kafofin yaɗa labarai na gargajiya da na sada zumunci |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma’ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| 24. **Taruwanni na sauraren kowa da kowa** | **Taruwanni na sauraren kowa da kowa** taruwanni ne inda ake gayyatar al’umma, inda shugabanni da ƴan ƙasa suna iya musanyar bayanai, su kuma bada ra’ayinsu game da al’amuran da suka shafi al’umma. Wannan taruwanni sun zama ɗaya daga cikin hanyoyin bincike daga wajen mutane. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar taruwanni na kowa da kowa, da ake tsarawa domin shugabannin ma’aikatun HKLJH a dukan matakai na tsari da projen HKLJH;<br>• Ana yin wannan taruwanni na kowa da kowa (inda akwai kasancewar gungun marasa galihu, kamar mata, da matasa, nakkasassu matalauta) lokaci zuwa lokaci, ana kuma yaɗa cikin ma’aikatun kiyon lafiya da tsarin HKLJH |
| 25. **Sanarwa gaban kowa a kan kuɗin da aka kashe** | **Sanarwa a kan kuɗin** da aka kashe, shi ne a bayyana ma mutane a fili irin yadda gwamnati take kashe kuɗi, domin a yardar ma ƴan ƙasa su nemi gwamnati ya bada lissafi a kan yadda ya kashe kuɗin. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar sanarwa a fili a kan kashe-kashen kuɗi da ya shafi HKLJH cikin dukan waɗanda suka sa hannu cikin aiki a dukan matakai na shugabanci ma’aikatun kiyon lafiya, da tsarin HKLJH<br>• Sanarwa a fili na kuɗin da aka kashe cikin aikin HKLJH lokaci zuwa lokaci, da kuma yaɗa labari ta hanyar kafofin sadawar na gargajiya, da na sada zumunta<br>• Tsara taro na kowa da kowa a matakai daban daban, tare da sa hannu duk wanɗanda aikin ya shafa, cikin fannin HKLJH da kuma gungun marasa galihu, domin a yi musanyar bayanai a kan abin da sanarwar ta ƙumsa akan kuɗin da aka kashe, da bada shawarwarin da suka kamata<br>• A shirya kundin neman afuwa tare da dukan masu sa hannu a cikin aikin HKLJH bayan da an yi sanarwa a fili game da sha’anin kashe kuɗi da kuma taron tattaunawa |
| 26. **Bincike da al’umma ke yi** | **Bincike da al’umma ke yi** shi ne hanyoyin da ake bi domin a tattara bayanai a kan tsarin proje, inda ake nazarinsu, ake kuma raba su zuwa ga kowa. Mambobin al’umma suna aikin bincike, wanda daga ƙarshe za a raba | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar binciken da al’umma ke yi a cikin masu sa hannu cikin aikin HKLJH<br>• Tsara binciken da al’umma ke yi cikin ma’aikatun kiyon lafiya ko tsari da projen HKLJH, da kuma yaɗa sakamakon ta kafofin sadarwa na gargajiya da na sada zumunta |

| Hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa | Ma’ana | Yadda ake aiki da hanyar cikin HKLJH |
|---|---|---|
| | sakamakon, a kuma tattauna a kai cikin taro. | |
| 27. **Komitin masu amfana da aikin** | **Komitotin tafiyar da aiki na masu amfana da aiki,** su ne gungun mutane da suke amfana da aiki, kuma suke da matsayin tafiyar da aiki zuwa nan gaba, domin a kafa, a tafiyar da wasu ayuka. Gurin waɗannan komitoti shi ne bunƙasa sa hannun, bada lissafi da binciken al’amarin kuɗi. | • A fassara kuma a yaɗa ma’anar komiti masu amfana da aikin HKLJH, cikin al’umma da ƙungiyoyin fara hula, a dukan matakan shugabancin ma’aikatun kiyon lafiya<br>• A sa wannan komiti ya yi aiki yadda ya kamata, aiki mai ɗorewa, mai shafar kowa da kowa ta fannin aikin HKLJH , masamman cikin matuane marasa galihu ko da aka ware cikin birni da ƙauye<br>• A wallafa rahotanni na bin sau-da-ƙafa a kan aiki komitoti, a kuma yaɗa su cikin dukan waɗanda ke da sa hannu cikin aikin HKLJH<br>• A tsara taron tattaunawa na kowa da kowa a kan rahoton komitotin masu amfana da aikin HKLJH, a kuma yaɗa shi cikin kafofin yaɗa labarai |

## 6. Auna muhimmancin ɗaukar niyya game da tsari/projen HKLJH

Domin a iya yin zaɓe mafi kyau game da ɗaukar niyyar da ta dace domin tafiyar da tsari ko proje na HKLJH , masu kula da tafiyar da tsarin HKLJH na bukatar su aza wa kansu wasu tambayoyi:

- Wace irin niyya ce ta ƴan ƙasa ta yi daidai da guri, da yanayin da tsari/proje HKLJH suke ciki?
- Dangance da irin niyyar ƴan ƙasa da aka zaɓa domin tafiyar da tsari/projen HKLJH, waɗanne hanyoyi ne suka fi muhimanci?
- Ina matsayin sa hannun gwamnati da ake bukata domin a aiwatar da hanyar ɗaukar niyyar ƴan ƙasa da aka zaɓa?
- Ina matsayin sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki, da ake bukata domin a aiwatar hanyar ɗaukar niyyar ƴan ƙasa da aka zaɓa?
- Ina abin da ke da wuya, da irin sanin da ake bukata domin a aiwatar da hanyoyin ɗaukar niyyar ƴan ƙasa da aka zaɓa?
- Ko hanyar ɗauka niyyar ƴan ƙasa tana bukatar wani tsawon lokaci?
- Ko hanyar ɗauka niyyar ƴan kasa da aka zaɓa na bukatar a kashe kuɗi game da tsari/projen HKLJH?

Wannan allo yana nuna irin niyyar da gwamnati da ƴan ƙasa, ya kamata su ɗauka, da irin iyawa, da lokaci, da kuɗin da ake bukata domin a iya aiwatar da wata hanyar ɗaukar niyya.

Allon auna muhimmancin ɗaukar niyya domin tsarin/projen HKLJH

| Irin niyyar aka ɗauka | Hanyar ɗaukar niyya mai muhimmanci | Sa hannun gwamnati cikin aiki | Sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki | Wuyar aiki da iyawar da ake bukata | Lokaci | Farashe |
|---|---|---|---|---|---|---|
| **Neman shawara** | Taron kowa da kowa | Madaidaici | Kaɗan | Madaidaiciya | Kaɗan | Kaɗan |
| | Tattaunawa cikin gungun mutane | Kaɗan | Kaɗan | Madaidaiciya | Madaidaici | Madaidaici |
| | Masu neman shawara/ komiti | Madaidaici | Kaɗan | Madaidaiciya | madaidaici | Kaɗain |
| **Sauraren ƙara** | Hanyar kula da kan ƙara da aka yi | Kaɗan | Kaɗan | Madaidaiciya | Kaɗan | Kaɗan |
| | Ƴan ƙasa masu auna aiki | Madaidaici | Madaidaici | Madaidaiciya | Kaɗani | Kaɗan |
| **A tattara, a rubuce, sanar da gudummawar ƴan ƙasa** | Taron sauraren kowa da kowa | Madaidaici | Kaɗan | Madaidaiciya | Kaɗan | Kaɗan |
| | Tattaunawa cikin gungun mutane | Kaɗan | Kaɗan | Madaidaiciya | Madaidaici | Madaidaici |
| | Binciken samun gamsuwa | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |

| Irin niyyar aka ɗauka | Hanyar ɗaukar niyya mai muhimmanci | Sa hannun gwamnati cikin aiki | Sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki | Wuyar aiki da iyawar da ake bukata | Lokaci | Farashe |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | Katin auna aiki na al'umma | Madaidaici | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Allon auna ayuka na al'umma | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Madaidaiciya | Da yawa | Mai tsada |
| **Ɗaukar kuduri tare** | Kasancewar ƴan ƙasa/masu amfana cikin rukunin masu ɗaukar ƙuduri | Madaidaici | Madaidaici | Madaidaiciya | Madaidaici | Kaɗan |
| | Wa'adin aiki da sahihanci | Mai ƙarfi | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan |
| | Tsara aiki tare | Madaidaici | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Shirya kasafin kuɗi tare | Mai ƙarfi | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Ƴan ƙasa masu auna aiki | Madaidaici | Madaidaici | Madaidaiciya | Kaɗan | Kaɗan |
| **Bin sau-da-ƙafa da ƴan ƙasa suke tafiyar da shi** | Lura da saye-saye | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Da yawa | Madaidaici | madaidaici |
| | Lura da kashe-kashen kuɗi | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Madaidaiciya | Da yawa | Mai tsada |
| | Allon auna aiki na al'umma | Madaidaici | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Binciken da al'umma take yi | Madaidaici | Mai ƙarfi | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Katin auna aiki na ƴan ƙasa | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Madaidaiciya | Da yawa | Mai tsada |
| | Binciken samun gamsuwa | Madaidaici | Mai ƙarfi | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| **A ba ƴan ƙasa kayan aiki, da ikon amfani da su** | Tsara aiki tare | Madaidaici | Madaidaici | Da yawa | Da yawa | Mai tsada |
| | Tafiyar da aikin al'umma | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Da yawa | Da yawa | Madaidiaci |
| | Bada kwangila daga al'umma | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Da yawa | Da yawa | Madaidaici |
| | Bin sau-da-ƙafa tare | Mai ƙarfi | Mai ƙarfi | Da yawa | Madaidai ci | Madaidaici |
| **Ƙarfafa ɗaukar niyyar ƴan ƙasa** | Taron waye kai a kan kasafin kuɗi | Kaɗan | Madaidaici | Kaɗan | Madaidaici | Madaidaici |
| | Bada rahoton kuɗin da aka samu da wanda aka kashe | Madaidaici | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan |
| **Yaɗa labarai** | Taron bada bayanai | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan | Madaidaici | Madaidaici |
| | Kudayen ƴan ƙasa | Mai ƙarfi | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan |

| Irin niyyar aka ɗauka | Hanyar ɗaukar niyya mai muhimmanci | Sa hannun gwamnati cikin aiki | Sa hannun ƴan ƙasa cikin aiki | Wuyar aiki da iyawar da ake bukata | Lokaci | Farash e |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | Wuraren samun kulawa domin ƴan ƙasa | Mai ƙarfi | Kaɗan | Kaɗan | madaid aici | Madaid aici |
| | Yin kasafin kuɗi cikin haske | Mai karfi | Madaidaici | Kaɗan | madaid aici | Madaid aici |
| | Rahoton abin da aka samu da abin da aka kashe | Madaidaici | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan | Kaɗan |
| | Taron waye kai a kan kasafin kuɗi | Kaɗan | madaidaici | Kaɗan | Madaid aici | Madaid aici |
| | Nazarin kasafin kuɗi daga na waje | Kaɗan | Mai ƙarfi | Kaɗan | Da yawa | Madaid aici |
| | Kasafin kuɗi da ƴan ƙasa suka shirya | Mai ƙarfi | Madaidaici | Kaɗan | madaid aici | Madaid aici |

### 7. Maƙasudi

Wannan kundin koyaswa yana gabatar da niyyar ƴan ƙasa, tamkar hanyar da ake bukata domin tabbatar da cikakken sa hannu ƴan ƙasa, cikin tafiyar da tsari da projen HKLJH.

Kundi koyaswa yana bada hanyoyi ashirin da bakwai (27) da ake iya amfani da su cikin aikin HKLJH bisa ga yanayi na masamman da ake ciki.

Muna fatan cewa yaɗa zancen niyyar ƴan ƙasa cikin ma'aiktan HKLJH zai sa ƴan ƙasa su sa hannu sosai cikin shugabancin ma'aikatun kiyon lafiya, da cikin tafiyar da tsari, da projen kiyon lafiya ta fannin jima'i da haifuwa.

Abubuwan da ake iya dubawa

https://www.larousse.fr/dictionnaires/francais (consulté le 20 Août 2019)

International Association for Public Participation. *The Spectrum of Public Participation*. Australia: 2014.

The World Bank Group (WBG). *STRATEGIC FRAMEWORK FOR MAINSTREAMING CITIZEN ENGAGEMENT IN WORLD BANK GROUP OPERATIONS: Engaging with Citizens for Improved Results.* USA: 2013.